# Lallai ni ina jiye muku tsoro a baya na, abinda za'a buɗe muku na ƙawar duniya da adonta

Daga Abu Sa'id al-Kudri - Allah Ya yarda da shi -: Cewa Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya zauna wata rana akan minbari muma muka zauna a gefensa, sai ya ce: "Lallai ni ina jiye muku tsoro a baya na, abinda za'a buɗe muku na ƙawar duniya da adonta" sai wani mutum ya ce: Ya Manzon Allah, shin alheri yana zuwa da sharri ne? sai Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya yi shiru, sai akace masa: Meke damunka ne? kana yi wa Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - kuma bai kulaka ba ? sai mukaga cewa can ana saukar me (da wahayi) ne? ya ce: Sai ya shafe gumi daga gare shi , sai ya ce: "Ina mai tambaya?" kamar shi ya yabe shi , sai ya ce: "Lallai alheri ba ya zuwa da sharri, yana daga abinda kaka take tsirarwa (akwai) abinda yake kashewa ko ya aibata, sai masu cin ciyayi, sun ci har saida kwiɓinansu suka cika sai suka fuskanci idan rana, sai suka yi toroso suka yi fitsari, suka yi kiwo, lallai wannan dukiyar koriyace mai zaƙi, madalla da na musulmi abinda aka bawa miskini daga gareta da maraya da ɗan matafiyi - ko kamar yadda Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata ya ce -: Kuma cewa shi wanda ya ɗauketa ba tare da haƙƙinta ba, to kwatankwacinsa kamar wanda yake ci ne ba ya ƙoshi, zata zama mai yi masa shaida ranar alƙiyama".

[Ingantacce ne] [Bukhari da Muslim suka Rawaito shi]

Wata rana Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya zauna akan minbari yana karantar da sahabbansa sai ya ce: Lallai cewa mafi yawancin abinda nake jiye muku tsoro a bayana (shi ne) abinda za'a buɗa muku na albarkatun ƙasa da ƙawace-ƙawacen duniya da adonta da kyanta, da abinda ke cikinta na nau'ikan jin daɗi da tufa da shukoki da wasunsu daga abinda mutane suke alfahari da kyawunsu tare da ƙarancin wanzuwa. Sai wani mutum ya ce: Kawace-ƙawacen duniya ni'imace daga Allah, shin wannan ni'imar zata dawo ta zama azaba da uƙuba?! Sai mutane suka zargi mai tambayar yayin da suka gan shi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya yi shiru, suka zaci cewa ya fusatar da shi ne. Sai ya bayyana cewa shi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya kasance wahayi yana saukar masa ne, sannan ya fara shafe gumi daga goshinsa, sai ya ce: Ina mai tambaya? Ya ce: Ni ne. Sai ya godewa Allah ya yi yabo a gareShi, sannan tsira da amincin Allah su tabbata agare shi ya ce: Alheri na haƙiƙa ba ya zuwa da (komai) sai da alheri, sai dai waɗannan ƙawace-ƙawacen ba tsantsar alheri bane saboda abinda suke kaiwa gare shi na fitina da gasa da shagaltuwa da su daga cikar fuskantar lahira, sai ya buga misali ga hakan sai ya ce: Lallai tsiron kaka da korensa, shi wani nau'i ne na shuka da yake ƙayatar da dabbobi sai ya yi kisa dan yawan ci da cikaciki ko ya kusa yin kisa, sai (dabba) mai cin koriyar ciyawa ta ci har ta cika kwiɓinan cikinta, sai ta fuskanci rana ta yi toroso daga cikinta a sirance ko ta yi fitsari,

sannan ta nemi daga abinda ke cikin hantarta sai ta tauna shi sannan ta hadiye shi, sannan ta dawo sai ta cinye. Domin cewa wannan dukiyar kamar maɓungura ƙasane koraye mai zaƙi, yana kisa ko yana kusa ya yi kisa saboda yawansa; sai dai idan ya taƙaita daga gare shi akan kaɗan ɗin da buƙatuwa take isa zuwa gareshi, kuma isuwa take samuwa da shi ta hanyar halal domin cewa shi ba ya cutarwa, madalla dana musulmi wanda shi ga wanda ya ba wa miskini da maraya da matafiyi daga gareta, wanda ya karɓeta da haƙƙinta za'a yi masa albarka a cikinta, wanda ya karɓeta ba tare da haƙƙinta ba to kwatankwacinsa kamar kwatankwacin wanda yake ci ne ba ya ƙoshi, kuma zata zama mai shaida akansa a ranar alƙiyama.

https://sunnah.global/hadeeth/ha/show/4180